# Surah 93: Al-Duha - سورة الضحى

بسم الله الرحمن الرحيم

[93:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

وَالضُّحَىٰ ﴿١﴾

[93:1] Ina rantsuwa da hantsi.

وَاللَّيْلِ إِذَا سَجَىٰ ﴿٢﴾

[93:2] Da dare a lokacin da ta fadi.

مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ﴿٣﴾

[93:3] Ubangijinka bai manta da kai ba, kuma bai qi ka ba.

وَلَلْآخِرَةُ خَيْرٌ لَّكَ مِنَ الْأُولَىٰ ﴿٤﴾

[93:4] Kuma Lahira ce mafi alheri a gare ka da wannan farkon (*rayuwan*).

وَلَسَوْفَ يُعْطِيكَ رَبُّكَ فَتَرْضَىٰ ﴿٥﴾

[93:5] Kuma, Ubangijinka zai ba ka kyauta; ka yi farin ciki.

أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَآوَىٰ ﴿٦﴾

[93:6] Shin, bai same ka maraya ba, sa'an nan Ya baka gida?

وَوَجَدَكَ ضَالًّا فَهَدَىٰ ﴿٧﴾

[93:7] Ya same ka batacce, sai Ya shiryar da kai.

وَوَجَدَكَ عَآئِلٗا فَأَغۡنَىٰ ٨

[93:8] Ya same ka matalauci, sai Ya wadata ka.

فَأَمَّا ٱلۡيَتِيمَ فَلَا تَقۡهَرۡ ٩

[93:9] Saboda haka, kada ka manta da maraya.

وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنۡهَرۡ ١٠

[93:10] Kada ka yi wa almajiri, tsawatawa.

وَأَمَّا بِنِعۡمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثۡ ١١

[93:11] Kuma ka zayyana ni'imar Ubangijinka da ya yi a kanka.